## EPISODE 26

**<u>Characters</u>**

***Tina***

***Hannah***

***Danjuma***

***Laraba***

***Dr. Daoud***

---

**Scene 1**

**Northern Kaduna, Kande's House.**

1. **MUSIC:** **<u>THEME MUSIC</u>**
2. **SFX:** **<u>SOUND OF A KNOCK ON THE DOOR</u>**
3. **SFX:** **<u>SOUND OF DOOR OPENING</u>**
4. **HANNAH:** **(SHOCKED)** Tina me kike yi a nan, marasa kunya?
5. **TINA:** Oh! Hannah, ki kwantar da hankalinki domin ba kumburarren fuskarki ne na zo gani ba.
6. **HANNAH:** Toh me ya kawo ki gidan mahaifiya ta? Ni dai ban gayyace ki ba.
7. **TINA:** Don Allah Hannah ki daina yi kamar ke mutumiya ce mai amfani. Kamar yadda na ce, ban zo ganin ki ba. Gwaggo Kande ce ta aika a kira ni. Ina fata ba da*d*ewa zamu yi ba, domin ina aiki dayawa kuma masoyi na Danjuma na jira na.
8. **HANNAH:** **(FURIOUSLY)** Ki yi shiru, wawiya kawai! Marasa ladabi kamar ki. Ina tir da ranar da dauke ki cikin gida na, marasa godiya!
9. **TINA:** Ahap, Allah Sarki Hannah! Me yasa kike damun kanki ne? Baki gani cewa duk maganganunki basu yin shaida a jiki na? Bana iya gane abun da kike fa*d*i ma. Saboda haka ki share!
10. **HANNAH:** Ta yaya zaki ji abun da nake fa*d*a bayan ke shai*d*aniya ce mai munafurci? Marasa kunya kawai! Jaka!

11. **TINA:** **(LAUGHING, IRRITATED)** Hannah, Hannah! Matar Danjuma ta jiya! Gwara ki yarda cewa shi ba naki bane kuma domin lafiyar *d*an da kike *d*auke da.

12. **HANNAH:** **(FURIOUS)** Tina, ke wawiya ce. *B*arauniyar miji!

13. **SFX:** **<u>SOUND OF A SCUFFLE AS BOTH WOMEN TRYING TO FIGHT</u>.**

14. **HANNAH:** Tina zan koya miki hankalin da zaki yi ba*k*in cikin wannan mugun wasa da kika yi da ni. Baza ki *k*ara yi ma wani ba kuma har *k*arshen rayuwarki.

15. **TINA:** Hannah abun tausayi ne cewa baki koya yadda ake ri*k*e miji ba, shi yasa Danjuma yake so na fiye da ke. **(LAUGHING)** Kin gani ko, ba laifi na bane da kika rasa shi. Wasu matan sun fi wasu, sun fi su sosai ma. Ai kin gane abun da nake gaya miki.

16. **SFX:** **<u>SOUND OF FOOTSTEPS AS DANJUMA STEPS OUT TO CONFRONT TINA.</u>**

17. **DANJUMA:** **(CLAPPING HANDS)** O-ho Tina. Me yasa kika daina magana? Kina da abubuwan fa*d*i ko? Don Allah ki cigaba.

18. **TINA:** **(SHOCKED, STAMMERING)** D-d-d-danjuma! Menene kake yi a nan? Ba ya kamata kana ofis ba?

19. **SFX:** **<u>SOUND OF KANDE'S FOOTSTEPS, ALSO STEPPING OUT.</u>**

20. **TINA:** **(SHOCKED, STAMMERING)** Me?! Gwaggo Kande! Ke ma kina nan? A-a-amma Hannah ta ce wai kin fita!

21. **DANJUMA:** Shi yasa kika nuna halinki na gaske ko Tina? Yaya kika yi wa ni da Hannah haka? Laifi muka yi da muka rike ki?

22. **TINA:** Wayyo, na gama, na lalace!

23. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**Scene 2**

*Northern Kaduna. Health Centre.*

24. **SFX:** **<u>SOUNDS OF ROAD AMBIENCE IN THE DISTANCE</u>**

25. **LARABA:** **(UNCOMFORTABLE)** Dr. Daoud, zan iya kwashe katunan marasa lafiya yanzu? **(PAUSES)** Dr. Daoud, baka amsa ba.

26. **DR. DAOUD:** Eh Nas Laraba? Menene?

27. **LARABA:** **(ANGRY)** Kalli nan Dr. Daoud, na san cewa babu da*d*i aiki tare da kai saboda tarihin dangantakarmu, amma ya kamata mu yi kokari mu yi aikinmu kamar yadda ya kamata. Ba zaka iya guduwa daga gare ni a asibiti domin kana ba*k*in ciki dangantakarmu ya warware ba. Dole ne mu yi aikin mu tare.

28. **DR. DAOUD:** **(BITTERLY)** Kin yi magana mai kyau Nas. Abun da kika zo ki gaya mun kenan a ofis na?

29. **LARABA:** **(UPSET)** Manta kawai Dr. Daoud. Na zo ne na tambaye ka game da katunan marasa lafiya, amma ba sauri ake yi ba. Zan iya dawowa anjima idan aiki ne yayi maka yawa yanzu.

30. **DR. DAOUD:** Tsaya Laraba, don Allah. Kafin ki tafi, ina son na tambaye ki wani abu.

31. **LARABA:** Na'am Likita, menene?

32. **DR. DAOUD:** Don Allah ki zauna.

33. **SFX:** **<u>SOUND OF CHAIR BEING DRAGGED ON THE FLOOR AND CREAKING AS LARABA SITS</u>**

34. **LARABA:** Menene Likita?

35. **DR. DAOUD:** **(SERIOUS)** Laraba, na ji wasu maganganu game da tarihinki. Ban san cewa kin ga ba*k*in ciki sosai kaman haka ba.

36. **LARABA:** **(BITTERLY)** Eh, ina ganin duk asibitin ya ji maganar tarihi na a makonnin da suka gabata. *K*ila ma dukkan Kaduna ne ya ji cewa ina da rashin sa'a. Domin diramar mu da Asabe ya zama abun magana wa tsawon lokaci me yawa.

37. **DR. DAOUD:** Amma yaya ban sani ba? Yaya baki gaya mun ba, eh Laraba na?

38. **LARABA:** Rashin sa'a ba abun da za'a yi gadara dashi bane.

39. **DR. DAOUD:** Amma da kin gaya mini. Da ban ji wasu Nas na maganar ba da safen nan, ai da ban san komai ba! Ban ji da*d*in abun da ya faru tsakaninmu ba, musamman yadda kika *k*i ni Laraba.

40. **LARABA:** **(CALMLY)** Likita, don Allah kar ka fara wannan. Wannan ba wajen da zaka yi maganar nan bane.

41. **DR. DAOUD:** Babu abun da zan fara. Ina son in nuna miki yadda nake jin ba*k*in ciki, ina nufin nisantar mu, da rashin maganar mu, da dai komai-da-komai. *K*in da kika yi mini ya dame ni sosai har ya sa ina guduwa daga gare ki.

42. **LARABA:** **(SMILING)** Likita kenan*.* Na lura da komai, daga yadda kake *k*in amsa gaisuwa na, har da ka nemi wani likita ya *d*auki matsayinka a asibiti.

43. **DR. DAOUD**: **(CONFUSED)** Gani na yi shine ya fi. Amma abun da ban gane ba shine, laifin menene na yi miki da kika juya mini baya? Ina ta tunani amma na kasa ganewa.

44. **LARABA:** Babu abun da kayi mini. **(SADLY)** Kawai na tuno da rashin sa'an da ka fuskanta, idan ya ha*d*u da nawa kuma… sai na ji tsoro kar ya *b*ata mana rayuwarmu.

45. **DR. DAOUD:** Menene ya tabbatar miki da zamu samu mumunar rayuwa? Ba haka rayuwa take. Zai zamanto da duk wuyan da muka sha a rayuwa, wannan shine zai zama mana hanyar samun kwanciyar hankali, mu samu sabuwar rayuwa!

46. **LARABA:** **(AGREES)** Kana da gaskiya Daoud, *k*ila lokaci yayi mu samu kwanciyar hankali. **(RELIEVED)** Ah! Yanzu na samu sakewa, domin na yanke shawarar zan gwada more rayuwata.

47. **DR. DAOUD:** Ina son na zama wanda zai sa ki ji da*d*i masoyiyata.

48. **LARABA:** Oh Daoud. Na yi wa kai na al*k*awarin mantawa da baya. Abun da ya wuce, ya riga ya wuce. Ina fatan kyakkyawar rayuwa nan gaba.

49. **DR. DAOUD:** (**HAPPILY**) Alhamdulillah*!* **(EAGERLY)** Idan zan iya tambaya, mutane na suna iya zuwa wajen iyayenki?

50. **LARABA:** **(SHYLY)** Zasu iya mana.

51. **DR. DAOUD:** Ah! Masha Allah! Alhamdulillah! Ina da kwatancen gidan kawunki a Zaria. Zan je na fara daga wajensa ba tare da *b*ata lokaci ba.

52. **LARABA:** **(LAUGHS SHYLY)** Ah da sauri haka Daoud?

53. **DR. DAOUD:** **(LAUGHING)** Bai yi sauri ma haka ba. Da ace zan iya ne, da na je yau-yau ma, amma sai na tuntube iyali na domin su shirya.

54. **LARABA:** Mamana, Hajiya Lantana zata yi farin ciki sosai. Tana ta goyon bayanka tuntuni.

55. **DR. DAOUD:** **(EXCITED)** Heh Laraba, ina Allah-Allah mu fara rayuwarmu tare mu samu yara. Ina son ki matu*k*a.

56. **LARABA:** **(SMILING, SHYLY)** Likita kenan. Kar ka damu, yaran zasu samu komai na rayuwa da yardan Allah. Amma zamu yi tazzara tsakaninsu saboda dukkanmu zamu more rayuwarmu.

57. **DR. DAOUD:** **(AGREES, LAUGHING)** Na'am madam! Zamu yi nuni da rayuwarmu, za'a san mu da amfani da hanyar tazzaran haihuwa ta zamani.

58. **LARABA:** **(AGREES)** Eh, abun da zamu yi kenan Laraba ta.

59. **DR. DAOUD:** **(CUTS IN)** Kuma zamu tabbata cewa bayan muna more ingancin tazzaran haihuwa, zamu ringa gaya wa mutane duk amfanin da muke samu daga gare shi.

60. **LARABA:** **(LAUGHING, TEASING)** Mhmmm, ina jin ki "Dr. Tazaran Haihuwa"!

61. **DR. DAOUD:** **(LAUGHING, THEN SERIOUS)** Amma fa Laraba, ban ta*b*a sanin zan sake yin farin ciki a rayuwa ta kuma ba!

62. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**Scene 3**

*Northern Kaduna. Kande's House. Afternoon.*

63. **SFX:** **<u>SOUND OF SITTING ROOM AMBIENCE. RANDOM MUSIC PLAYING SLOWLY IN THE BACKGROUND.</u>**

64. **DANJUMA:** **(SURPRISED)** Hmmm Hannah, masoyiyata, ban ta*b*a tsammani Tina zata iya buga *k*arya kamar haka ba a kai na. Ah! Lalle!

65. **HANNAH:** **(CUTS IN)** Ina mamaki da ta yarda cewa ta baka magani ne saboda na zo na kama ku tare a *d*akinmu.

66. **DANJUMA:** Ah dole da yarda fa Hannah. Baki ga yadda Gwaggo Kande da kawunki suka bu*d*e mata ido ba? Gaskiya yayi ta zubowa daga bakinta kawai!

67. **BOTH:** **(LAUGHING)**

68. **DANJUMA:** **(APOLOGETIC)** Hannah, na ranste miki, ban san komai akan abun da tayi ba. Ban ma tuna da komai ba har yanzu. Amma na san cewa bani da hannu a cikin zargin, na ranste.

69. **HANNAH:** Toh, ka dai ji abun da ta fa*d*a a gidan. Ta ce wai ta ji kishin yadda muke zaman rayuwarmu ne, shine ta so ya zama nata.

70. **DANJUMA:** **(AMAZED)** Ah! Amma rayuwa na da ban tsoro. Da duk abun da muka yi ma Tina, me yasa zata biya mu da wannan?

71. **HANNAH:** Amma dai mun gode Allah ta fa*d*i gaskiya a gaban su Mama da Kawu Bala. In ba haka ba, babu wanda zai yarda da mu. Za'a ce wai mun yi wa yarinya sharri domin mu ma'aurata ne.

72. **DANJUMA:** Haka ne fa. Sa'a na shine mamanki ta yarda dani shi yasa ta kira kowa domin a warware maganar. Idan ba haka ba ai da na mutu!

73. **HANNAH:** Nima na yarda da ke, kawai dai na ru*d*e ne, musamman da na ganka kana kwance a gado kana barci bayan…

74. **DANJUMA:** **(CUTS IN)** Haba Hannah! Ki daina maganar. Ni ban tuna cewa wani abu ya faru ba. Ina son ke ma ki manta da abun. Babu abun da ya faru!

75. **HANNAH:** **(CALMLY)** Kana da gaskiya masoyi na. Hmm amma Danjuma, Tina ta same mu fa. Tayi niyyar karya iyalinmu, amma Alhamdulillah bata samu nasara ba.

76. **DANJUMA:** Amma ta kusa fa, da na rasa ki.

77. **HANNAH:** **(GUILTLY)** Amma bata ci nasarar raba mu ba. **(APOLOGETIC)** Danjuma, ka yi hakuri da na *k*i saurara maka.

78. **DANJUMA:** **(APOLOGETIC TOO)** Ni ma ina neman gafara da kika sha wuya haka. Na san cewa ba don dabarar da Tina ta ha*d*a ba, da baki yarda da maganar ta akan nawa ba.

79. **HANNAH:** **(SMILING)** Ina son ka Danjuma. Ita kuma Tina, ka bar maganar ta wa manya a *k*auye. Ta san sakamakon laifin da ta yi, kuma na san sai an hukunta ta.

80. **DANJUMA:** (**AGREES)** Toh*,* ita ta janyo ma kanta. Sai ta fuskance shi ita ka*d*ai.

81. **HANNAH:** **(APOLOGETIC TOO)** Ka yi hakuri masoyi na. da ban yi shakkan ka ba.

82. **DANJUMA:** **(SMILING)** Babu komai, lamarin Tina ya koya mana darasi; baza mu sake shakkan junanmu ba. Musamman ma, mu yarda da junanmu mu ringa tattauna komai-da-komai a matsayinmu na mata da miji, komin zafin maganar.

83. **HANNAH:** Da na saurara maka. Duk da haushin da na ji, da na ji gefenka kafin na yanke shawara.

84. **DANJUMA:** Kin san menene Hannah, duk abun da ya faru a rayuwar mutum ya kamata ya zama mishi darasi. Mu dai mun koyi darasi daga wannan abun kuma ba zamu *k*ara yin irin wannan kuskuren ba.

85. **MUSIC:** **BRIDGE MUSIC**

**Scene 4**

*Northern Kaduna. Danjuma's House. Evening***.**

86. **SFX:** **SOUND OF HAUSA MUSIC PLAYING SOFTLY IN THE BACKGROUND**

87. **HANNAH:** **(EXCITED, CLAPPING HANDS TOGETHER)** Ah, Laraba! Kai!

88. **LARABA:** Da gaske ne fa Hannah. Na fi son *k*aramin biki. Bana son jama'a suyi yawa, alkhairin Allah kawai nake nema.

*89.* **HANNAH:** Kina da gaskiya. Babbar bukata kenan, domin baka san inda ma*k*iyi ke *b*oyewa ba. Kinga sha'ani na da Tina ai?

90. **LARABA:** **(AGREES)** Ohoo*!* Ashe kin gane. Banda ma wannan, ai na tsufa ma wata biki.

91. **HANNAH:** Baki tsufa ba fa. Na ga, kuma na ji labarin manya dayawa masu yin shagali sosai a bikinsu. Saboda haka kar ki yi maganar tsufa a nan.

92. **LARABA:** Gaskiya, ina son in kawad da wani abun kunya kamar fasawar auren, kamar yadda ya faru da Jallo.

93. **HANNAH:** **(CUTS IN)** Ki kwantar da hankalinki mana. Duk wannan ba zai sake faruwa kuma ba, In Sha Allah. Kar ki manta kuma cewa Jallo bai fasa aurenki ba, lokacin shi ne ya zo kawai. Saboda haka, ba son sa bane.

94. **LARABA:** Na sani, shi yasa nake son *k*aramin biki. In da so ma, a yi a kotu.

95. **HANNAH:** **(CUTS IN)** Laraba don Allah ki daina irin wannan maganar. Na gaya miki babu abun da zai faru, da Yardan Allah.

96. **LARABA:** Toh fa Hannah, ina addu'a komai ya je daidai.

97. **HANNAH:** Amin. **(HAPPILY)** Yanzu kike magana. Ki yi murnar ki kawai ki daina damuwa da gobe. Yana Hannun Allah.

98. **LARABA**: Na'am Madam! Na ji da*d*i da shirye-shiryen bikin wallahi. Duk da maganar da nake yi na *k*aramin biki, na san cewa kawu na da Mama Lantana ba zasu yarda da wannan ba.

99. **HANNAH:** Yauwa, gwara da kika tuna cewa akwai 'yan-uwa dayawa da ba zasu yarda ba. Ni kaina ba zan yarda ba.

100. **LARABA:** Ah! Me zaki yi?

101. **HANNAH:** Kawai zan gaya wa 'yan-uwa su *k*i maganrki.

102. **LARABA:** **(LAUGHING)** Hannah ke muguwa ce wani lokaci, gaskiya.

103. **HANNAH:** Laraba, idan akwai wanda ta cancanta ta samu ta ji da*d*in bikinta, ke ce. Ya dace ki more rayuwarki cikin farin ciki.

104. **LARABA:** **(SHYLY)** Abun da Daoud ya ce kenan da na gaya masa batun aure a kotu. Bai son ya ji maganar ma. Ya ce yana son na ji da*d*in biki na kamar kowacce mace, tunda ban samu ba can baya.

105. **HANNAH:** **(TEASING)** Hmmm Laraba, kina da sa'a! Kamar saurayin nan naki na son ya kashe ku*d*i akan ki. Kuma yana nuna miki so!

106. **LARABA:** Ah Hannah, ina godiya fa sosai. Shi mutum ne me kirki. Ina da sa'a matu*k*a. **(SHYLY)** Kuma ina son sa sosai!

107. **HANNAH:** **(SERIOUS)** Haka ya kamata ya zama Laraba. Ina miki murna *k*awa ta. Na san cewa lokaci yayi ki yi fara'a a rayuwarki.

108. **LARABA:** Yauwa, yaya abubuwa suke tsakaninki da Danjuma yanzu?

109. **HANNAH:** **(REMORSE)** Muna ta *k*o*k*arinmu. Bamu son hakan ya sake faruwa. Ba za'a yi wasa da sha'anin ma'aurata su ringa tattaunawa tare da junansu ba. Yana da inganci sosai Laraba.

110. **LARABA:** Haka ne *k*awa ta. Shine sirrin zamar lafiyan aure, ko ba haka ba?

111. **HANNAH:** Gaskiya Laraba. Yana da tasiri ga ma'aurata su ringa sauraran junansu, su ba wa junansu damar yin bayani ba tare da wata zato ba da zai jawo musu matsala.

112. **LARABA:** Zan yi iya *k*o*k*ari na Hannah, na yi miki al*k*awari.

113. **HANNAH:** **(PLEADING)** Don Allah kiyi fiye da iya *k*o*k*arinki. **(GUILTLY)** Domin shine abu guda *d*aya da yake sani na ji kunya kowacce rana. Ina ganin kaman ban yi *k*o*k*arin hana Tina shigowa tsakani na da Danjuma, har ya kusa ya kawo mutuwar aurenmu.

114. **LARABA:** Mun gode wa Allah hakan bai faru ba. Kamar dai yadda na ce, zan zama mata mai kirki, mai ganewa da Daoud. Na san hakan zai taimaka mu samu rayuwa mai inganci.

115. **HANNAH:** Abun da kuke bu*k*ata kenan. Idan mata da miji na da ha*d*in kai suna yanke shawarwari masu muhimmanci ga rayuwarsu, dole ne su samu rayuwa mai kyau.

116. **LARABA:** Hmm Hannah, ina mamaki da na sake na zo wannan shafi a cikin rayuwa ta. Ban ta*b*a tsammani zan iya sa rai akan rayuwa ta na gobe ba.

117. **MUSIC:** **THEME MUSIC**.